# Taron Kawar *da duk* Nau'in Bambanci *ga* Mata



United Nations

A Translation of the "Convention on the Elimination of All Forms of Discrimination Against Women" into Hausa

## Gabatarwa

Taron kawar da duk nau'in bambanci ga mata, da babban zauren Majalisar Ɗunkin Ɗuniya ta amince da shi a 1979 an suranta shi da dokar duniya a kan haƙƙoƙin mata. Ya ƙunshi suranta shi da dokar duniya akan haƙƙoƙin mata. Ya ƙunshi muƙaddima da dokoki 30, yayi bayanin abin da ake kira nunin bambanci ga mata kuma ya shata wa ƙasashe hanyoyin da za a bi domin kawo ƙarshen wannan nunin bambancin.

Taron ya amince da cewa, nunin bambanci ga mata shi ne "... duk wani bambanci da ya ware ko taƙaita mata dangane da jinsinsu tare da fatar hana mata more rayuwarsu ba tare da la'akarin cewa masu aure ne ko marasa aure ba, a kan tafarkin daidaita maza da mata a haƙƙoƙin bil'Adama da cikakken haƙƙi da ya shafi siyasa, tattalin arziki, jin daɗi, al'adu, mata masu kayan sarki ne ko kuma fararen hula."

Don tabbacin amincewa da Taron, ƙasashen sun yi ƙudurin ɗaukar matakai iri-iri domin kawo ƙarshen nunin bambanci da duk rassansa, da suka haɗa da:

- daidaita maza da mata a fannin shara'a, kawar da duk sassan shara'a (dokoki) da suka nunawa mata bambanci tare da maye gurbin su da dokokin da suka dace da ke hana nunin bambanci ga mata;
- a kafa kotuttukan tafi da gidanka da cibiyoyi domin ba da kyakkyawar kariya ga mata a kan nunin bambanci; da
- a tabbata kawar da duk nau'in nunin bambanci ga mata da mutane, ƙungiyoyi da masana'antu ke yi.

Taron ya samar da hanyar daidaita haƙƙoƙi tsakanin maza da mata ta tabbata cewa mata sun sami dama daidai da takwarorinsu maza a fannin siyasa da sha'anin aiki- -da ya haɗa da daman su yi zaɓe ko su tsaya takara don a zaɓe su- -kai har ta fannin ilimi da sha'anin ƙwadago. Kasashen sun amince da ɗaukan matakan da suka dace da suka haɗa da yin dokoki da matakan wuccin gadi na musamman, domin mata su morewa haƙƙoƙinsu na bil'Adama da na 'yanci.

Wannan Taron shi ne kawai sulhun da ake da shi a kan haƙƙin bil'Adama wanda ya ƙarfafa wa mata haƙƙin haihuwa, tare da ɗaukar al'ada da ɗabi'a su kasance masu ta'asiri wajen raba wa maza da mata rawar da zasu taka, da kuma dangantaka tsakanin iyali. Ya tabbatar wa mata haƙƙin samun, sauya ko riƙe muƙaminsu na zama 'yan ƙasa ko kuma na 'ya'yansu. Kasashen da suke cikin wannan Taron sun amince da su ɗauki matakan da suka dace don hana yin safara da bautar da mata.

Kasashen da suka sa hannu ga wannan Taron ko suka amince da shi, doka ta ɗora masu haƙƙin yi aiki da dokokin da Taron ya shata. Har-ila-yau sun ɗauki alkawalin ba da bayanin matakan da kasar ta ɗauka a kan sulhun a ƙalla duk kowace shekara huɗu.

Taron, wanda ya fara aiki 3 da watan Satumba 1981, ya sami amincewar ƙasashen da ke cikin Majalisar Ɗunkin Duniya guda 152 tun daga 31 ga watan Mayu na 1996.

## Kasashen da suka amince da wannan Taron

Tuna cewa dokokin Majalisar Dunkin Duniya ya sabunta imanin da yake da shi a kan hakin bil'Adama, da ya kunshi mutunci da kimar mutun wajen daidaita hakkokin maza da mata,

Tuna cewa dokar Duniya kan hakin bil'Adama ya karfafa dokar nan da ta hana nunin bambanci, kuma ta tabbatar da cewa duk mutun ana haihuwar sa ne da 'yantacce da ke da haki daidai da kowa, kuma kowa na da damar morewa hakki da diyauci nan take, ba tare da nunin bambanci ko wanne iri ba, wanda ya hada da bambanci da ya shafi jinsi,

Tuna cewa duk kasashen da suka sanya wa alkawarin nan na hakkin bil'Adama hannu, suna da dawainiyar ganin cewa hakken maza da mata ne su ci gajiyar tattalin arziki, zaman takewa, al'adu, abin da ya shafi farar hula, da siyasa ba tare da wani ya kwari wani ba,

Mu sanya Taron duniya da aka kammala a karkashin inuwar Majalisar Dunkin Duniya a cikin zaciya da kafafenta na musamman da ke bunkasa daidaita hakkokin maza da mata,

Har-ila-yau mu tuna da abin da aka yauke shawara akai, ikirari da shawarwarin da Majalisar Dunkin Duniya da kafefenta na musamman suka amince da shi wanda ke tallata daidai takar hakkokin maza da mata,

Har yanzu ana nuna damuwa, domin duk da tanaje-tanajen da aka yi domin hana nunin bambanci, har yanzu ana cigada da nuna bambanci ga jinsin mata,

Tuna cewa nuna bambanci ga mata ya sabawa kudurin daidaita hakki da girmama mutuncin bil'Adama, ya zama cikas ga rawar da mata zasu taka daidai da ta takwarorinsu maza, a fannin siyasa jindadin jama'a tattalin arziki da al'adun rayuwar kasashensu, yana hana cigaban rayuwa ingantacciya ga al'uma da iyali, kuma yana tauye mata wajen gudun mawar da zasu taka a cikin kasarsu da al'uma,

Ana nuna damuwa cewa a lokacin talauci (rashi) mata sukan yi karancin samun abinci, kiwon lafiya, ilimi, horo, hanyoyin samun aiki da dai sauran bukatu,

Mun gamsu cewa kafa wata sabuwar hanyar tattalin arziki ta duniya a kan daidaito da adalci zai taimaka sosai wajen daidaita hakkokin maza da mata,

An karfafa cewa kawar da bambancin launin fata na kowanne iri, kabilanci, mulkin mallaka na gida da na waje, shishigi, wata kasa ta mamaye wata, taushe wasu, da shisshigi a cikin harkokin cikin gida na wata kasa yana da muhimmanci ga bunkasa jin dadin hakkokin maza da mata,

An karfafa cewa zaman lumana da tsaro a duniya, da kwantar da

zaman ɗar-ɗar, haɗin kan ƙasashen duniya ba tare da la'akari da al'adarsu ko ƙarfin tattalin arzikinsu ba, cikakkiyar kwance ɗamar yaƙi, musamman na abin da ya shafi kwance ɗamarar makaman ƙare dangi a ƙarƙashin wata muhimmiyar doka ta duniya, ƙarfafa dokokin adalci, daidaito, alaƙa kyakkyawa tsakanin ƙasashe, tsare haƙƙokin mutane da ke karƙashin mulkin mallaka na cikin gida da na waje wanda zai jawo har ga su kai ga mulkin kai, tsare mutuncin iyakar ƙasashen juna da 'yancinsu zai bunƙasa zaman lafiyar jama'a da ci gabansu a ƙarshe zai kai ga tabbataccen daidaito tsakanin maza da mata,

Mun gamsu cewa cikakken cigaban ƙasa, jin daɗin duniya baki ɗaya, da zaman lafiya yana bukatar mata su ba da matuƙar dugun mawarsu daidai da ta irin ta takwarorinsu maza a duk sassan rayuwa,

A cikin zuciyarmu mu na nan sane da irin rawar da mata suke takawa wajen kula da iyali, da bunƙasar al'uma wanda har yanzu basu samu isasshen amincewa ba. Muhimmancin haihuwa da rawar da uwa da uba ke ba da wa wajen tarbiyar yara na nan, mun dai san cewa gudun mawar da mata ke ba da wa a fannin shaƙatawa ba wai rauni ba ne, amma abin lura a nan shi ne tarbiyar yara na bukatar maza da mata kai har da al'u'ma baki ɗaya,

Mu na son ku sani cewa sauyin da aka samu a cikin aikace-aikacen maza na al'a'da da na mata a cikin, al'uma da iyalai ana bukatarsace domin cimma daidaito cikakkiya tsakanin maza da mata,

Don yin ƙudurin zartar da matakan da aka amince da su a wajen Taron kawar da bambanci ga mata an ɗauki waɗannan matakan da ake bukata domin kawar da nunin bambanci ga mata da duk rassansa,

An yi ittifaƙi a kan waɗannan:

## Sashe na I

*Doka ta 1*

Wannan Taron dai ya fassara "nunin bambanci ga mata" cewa shi ne duk wani bambanci, cire wa ko taƙaitawa da aka yi ga jinsin (mata) da niyar kawar da jin daɗin da mata ke yi ba tare da la'akari da masu aure ne ko marasa aure ba, a tafarkin daidaito tsakanin maza da mata, a fannin haƙƙoƙin bil'Adama da 'yanci a siyasa, tattalin arziki, mu'amala, al'ada. kasancewa farar hula ne ko kuma dai masu kayan sarki.

*Doka ta 2*

Kasashen da suka sanya wa wannan dokar hannu ta nunin bambanci ga mata da duk rassansa sun amince da su cimma wannan manufar ta bin duk hanyoyin da suka dace ba tare da ɓata lokaci ba domin tabbatar da

an kawar da duk wani nau'in nunin bambanci ga mata, don haka suka yi alkawarin:

(a) Su sanya dokokin da zai daidaita hakkokin maza da mata a cikin tsarin mulkinsu ko tsarin shara'a idan dama bai kunshe da hakan, da bin hanyoyin da doka ta amince da su za a tabbata cewa wannan hakar ta cimma ruwa;

(b) A yi amfani da hanyoyin shara'a da sauran matakai da suka hada da sanya takunkumi inda ya dace domin hana duk wani nau'i na nunin bambanci ga mata;

(c) A samu kariya ta shara'a da zata kare hakkoki mata daidai da ta takwarorinsu maza, a yi amfani da ingantattun kotunan tafi da gidanka da suran cibiyoyi domin ba da kariya ga mata ga duk wani nau'i na nunin bambanci;

(d) A guje wa duk wani aiki da ke nuna wa mata bambanci, kuma a tabbata cewa hukumoni da cibiyoyi suna yin aiki da wannan dokar;

(e) Mutane, da kungiyoyi ko kamfanoni su dauki matakan da suka dace domin kawar da nunin bambanci ga mata;

(f) A dauka matakan da suka dace, da suka hada da kirkiro doka, yiwa dokar da ake da ita gyaran fuska ko watsi da dokar, ka'idoji, al'a'adu da wasu tabi'o'i wadanda ke nuna bambanci ga jinsin mata;

(g) A soke duk wata dokar kasa wadda ke nunin bambanci ga mata.

Doka ta 3

Duk kasashen da suka sanya wa wannan dokar hannu (suka amince da ita), ana son su dauki matakai a duk wata hanya ta rayuwa musamman a fannin siyasa, jin dadin jama'a, tattalin arziki da al'adu, har-ila-yau matakan su kunshi tsarin shara'a domin tabbatar da cikakken cigaba da bankasar mata, duk wannan dai ya kasance don ya basu damar jin dadin hakkokinsu na bil'Adama da 'yanci daidai da takwarorinsu maza.

*Doka ta 4*

1. Kasashen da suka amince da wannan dokar har suka dauki wasu matakan wuccin gadi da niyar gaggauta ciyar da mata gaba har su daidaita da takwarorinsu maza kada a dauke shi a matsayin nunin bambanci (son kai) makar dai yadda wannan Taron ya amince da shi, amman ka da a dauke shi a karshe ya zama matakin son kai ko na nuna wa mata wani matsayi na daban; sai a bar aiki da wadannan matakan yayin da aka cimma manufar daidata mata da maza a wajen ma'amala (kula).

2. Haka matakan musamman da kasashe suka dauka da suka hada da wadanda ke cikin dokokin wannan Taron da aka yi niyar kare haihuwa ka da a dauke shi a dauke shi a matsayin nunin bambanci.

*Doka ta 5*
Duk ƙasashen da suka amince da ƙudurin wannan Taron zasu ɗauki matakan da suka dace:

(a) Za a yiwa tsarin ma'amala da al'adun maza da mata gyaran fuska domin tabbacin kawar da son kai, da duk miyagun al'adu da aka gina su kan ra'ayin ƙasƙanci ko ɗaukakan maza ko mata, ko kuma wani takammen aikin da aka keɓe domin mace ko namiji;
(b) A ingantar da tsarin ilimin iyali domin ya ƙunshi kyakkyawar fahimtar sha'anin haihuwa, domin maza da mata su fahimci tarbiyar yara nauyinsu ne baki ɗaya, su kuma fahimci cewa abin da yara ke ra'ayi da cigabansu shi ne babban aikin iyaye a duk hali.

*Doka ta 6*
Duk ƙasashen da suka amince da wannan dokar zasu dauki matakan da suka amince da suka haɗa da ƙirƙiro dokoki da zasu daƙusar da duk nau'in safarar mata domin sanya su karuwanci.

## Sashe na II

*Doka ta 7*
Duk ƙasashen da suka amince da wannan doƙar zasu ɗauki duk matakan da suka dace domin kawar da nunin bambanci ga mata a fannin siyasa, gudun mawa ga ƙasa da tabbatar da cewa mata sun sami haƙƙoƙi daidai da na 'yan'uwansu maza kamar haka:

(a) su jefa ƙuri'a a cikin duk sha'anin zaɓen da ya taso da ƙuri'ar jin ra'ayin jama'a, kuma su kasance masu damar su tsaya a zaɓe su ga duk irin muƙamin da suke so a ƙasa;
(b) su shiga cikin masu tsara shirye-shiryen gwamnatocin ƙasashensu, da jami'an da ke gudanar da shirye-shiryen gwamnatocin, kuma a basu muƙaman gwamnati a cikin ƙasa daidai da takwarorinsu maza;
(c) su kata rawa a cikin ƙungiyoyin da ba na gwamnati ba da ke kula da mu'amalar jama'a, da siyasar cikin ƙasa.

*Doka ta 8*
Duk ƙasashen da suka amince da ra'ayin wannan Taron zasu ɗauki duk matakan da suka dace da zasu daidaita mata da maza wajen wakiltar gwamnatocinsu a ƙasashen waje, haka a basu daman yin aiki a ƙungiyoyin duniya.

*Doka ta 9*
1. Kasashen da suka amince da ƙudurin wannan Taron zasu baiwa mata haƙƙi daidai da maza domin su mallaki, su canza ko su cigaba da rike haƙƙinsu na zama 'yan ƙasarsu. Har-ila-yau zasu tabbatar

cewa auren baƙi ko canjin ƙasar da mazajensu suka yi bai maida mace wadda bata da ƙasa ba ko kuma ya tilasta ta zama 'yar ƙasar da mijin nata ya koma.

2. Kasashen da suka sanya hannu ga dokar wannan Taron zasu baiwa mata haƙƙi daidai da na maza dangane da zaɓa wa 'ya'yansu ƙasashe (ƙasa).

## Sashe na III

*Doka ta 10*

Kasashen da suka sanya wa waɗannan dokokin hannu zasu ɗauki matakan da zasu dace domin kawar da bambancin da ake nuna wa mata, domin a tabbatar da cewa mata na da haƙƙi daidai da maza a fannin ilimi, domin a tabbata cewa an daidaita su da takwarorinsu maza:

(a) Za a ɗauki irin wannan matakin a fannin ilimin koyon sana'o'izasu samu kafar ƙaro ilimi domin samun takardun shedar difiloma a makarantu daban-daban a karkara kai har da birane, wannan daidaitawar tsakanin maza da mata a fannin ilimi zata ƙunshi kafin shiga makaranta, fasaha, sashen ƙwararru da takardar ilimi mai zurfi haka nan a duk nau'in ilimin koyon sana'o'i;

(b) Zasu sami damar mallakan tsarin karatu, jarabawa iri ɗaya, ƙwararrun malamai da suka dace, filin makaranta da kayan aikin da suka dace daidai da ta maza;

(c) Kawar da takaitawar rawan da maza ko mata zasu taka a duk matakai da siffofin ilimi ta ƙarfafa makarantun da ake sa ɗalibai maza da mata da sauran fannonin ilimi da zai taimaka domin cimma wannan manufar, musamman ta yin bitar littafan karatu da tsare-tsaren makaranta da bin hanyar karantarwa da ta dace;

(d) Haka nana mata su more wa kuɗin da ake bayarwa domin ƙaro ilimi da duk sauran tallafin da ake bayarwa domin ƙaro ilimi;

(e) Haka su more wa tsare-tsaren cigaban ilimi, da zai haɗa da yaƙi da jahilci da sauran shirye-shiryen koyon ilimi na manya, musamman shirye-shiyen nan da zasu tabbatar da cike giɓin da ake da shi tsakanin ilimin maza da na mata;

(f) A tabbatar da rage yawan 'yammata masu barin karatu kafin su kammala shi, kuma a shirya wa 'yammata da mata waɗanda suka bar makaranta tun kafin su kammala wata hanyar cigaba da iliminsu;

(g) Su sami dama irin ta maza da zasu taka rawa wajen wasanni, sha'anin motsa jiki da iliminsa;

(h) Su sami damar samun wani ilimi na musamman da bayanai da zai taimaka wajen lafiya da jin daɗin iyali, da zai haɗa da bayani da shawara a kan ilimin tsarin iyali.

*Doka ta 11*

1. Kasashen da suka amince da ƙudurin wannan Taron zasu ɗauki matakan da suka dace domin kawar da nunin bambancin da ake nuna wa mata a fannin aiki (na gwamnati ko na kamfani), za a tabbata cewa mata na da haƙƙi daidai da na takwarorinsu maza, musamman:
   (a) Damar yin aiki ta kasance wani haƙƙi na duk bil'Adama;
   (b) Haƙin samun aikin ya kasance daidai da na maza, kai har ya kasance sharuɗdan ɗaukan aiki ya zama babu bambanci (da na maza);
   (c) Haƙin zaɓen irin aikin da mata ke son yi kuma kowanne iri ne, haƙin ciyar da su gaba a wurin aiki, ya kasance suna da kariyar aiki da duk irin abin da mai wannan aikin yake da damar samu ga doka, haƙƙin mata ne samun horo a wuraren koyon aikin hannu da sabunta koyon aiki da zai haɗa da ilimi mai zurfi kan ayyukan hannu da sake ilmantar da su ta yadda iliminsu zai dace da zamani;
   (d) Mata su sami biya iri ɗaya da maza a wurin aiki, da duk wata moriya da aikin ke samarwa kai har da hanyar da ake bi a duba aikin ya zama daidai da na maza;
   (e) Mata su mallaki haƙƙi iri ɗaya da na maza musamman lokacin da suka yi ritaya, rashin aiki, rashin lafiya, tsufa da sauran tawayar da ke hana yin aiki, kai har da haƙƙin biyan kuɗin hutu;
   (f) Mata su mallaki haƙƙin kariyar lafiya da kyakkyawan tsaro ko kariya a lokacin da suke yin aiki, kai hadda karijar jikinsu da zai taïmake su wajen haihuwa.
2. Domin hana nunin bambanci ga mata domin kawai suna da aure ko abin da ya shafi haihuwa, kuma a tabbatar da cewa suna da cikakken 'yanci wurin aiki, don haka ƙasashen da suka amince da wannan Taron zasu ɗauki duk matakan da suka dace haka:
   (a) A hana sanya wa mata takunkumi, kora daga aiki domin ciki ko hutun zuwa haihuwa, ko kora daga aiki domin wai kawai suna da aure;
   (b) A gabatar da hutun zuwa haihuwa tare da albashi ko da wani nau'in tallafi ba tare da barin inda ake yin aikin ba, a kuma basu alawus-alawus na matsayi ko na kula da gida;
   (c) A ƙarfafa samar da alawu-alawus don kula da iyali (gida) yadda iyaye zasu iya ɗaukar ɗawainiyar gida a matsayinsu na ma'aikata (na gwamnati ko kamfani) ba tare da sun kasa ba a cikin sha'anin gudanar da rayuwar iyalansu, don haka a ƙarfafa bunƙasa alawus-alawus da suka shafi cigaban sha'anin yara;

(d) A baiwa mata kariya lokacin da suke da juna biyu a ire-iren ayyukan da ke da hadarin ga rayuwarsu.

3. Tsarin dokar kariyar da ke cikin wannan littafin dokokin Taron za a yi bitarsa lokaci-lokaci a kan hasken ilimin kimiyya da fasahar da ake da ita don sakewa, sokewa ko kuma a fadada ta kamar dai yadda ake ganin yana da muhimmanaci.

*Doka ta 12*

1. Kasashen da suka amince da dokokin wannan Taron zasu dauki matakan da suka dace domin kawar da bambanci ga mata a fannin kiwon lafiya domin a daidaita hakkokinsu daidai da takwarorinsu maza a sashen kiwon lafiya har da abin da ya shafi sha'anin tsarin iyali.
2. Duk da tanadin da sakin laya na 1 na wannan dokar yayi, kasashen da suka amince da dokar wannan Taron zasu tabbata cewa sun yi wa mata isasshen tanadi a lokacin da suke da juna biyu, lokacin da suke kebe (kusan haihuwa) da lokacin da suke reno kuma ayi masu dawainiyar kyauta inda ake ganin ya dace, haka a tabbatar suna samun abinci isasshe mai gina jiki a lokacin da suke shayarwa.

*Doka ta 13*

Kasashen da suka amince da wannan Taron zasu dauki duk matakan da suka dace domin kawar da nunin bambanci ga mata a sassan tattalin arzikin kasa da jin dadin jama'a domin tabbacin cewa an daidaita hakkokin maza da mata musamman:

(a) A wajen hakkokin iyali;
(b) Damar samun bashi daga banki;
(c) Damar taka rawa a sha'anin shakatawa da wasanni da duk fannin al'adar rayuwar al'umarsu.

*Doka ta 14*

1. Kasashen da suka amince da wannan Taron zasu yi la'akari da matsalolin da matan karkara suke fuskanta, da irin muhimmiyar rawar da suke takawa a fannin tattalin arziki da ta shafi rayuwar 'ya'yansu, har da aikace-aikacen da suke yi da ba'a biyansu komai, don haka za a tabbatar da cewa matan karkara sun amfana daga dokokin wannan Taron.
2. Kasashen da suka amince da dokokin wannan Taron zasu dauki matakan da suka dace domin kawar da nunin bambanci da ake nuna wa matan karkara, don a tabbatar da an daidaita hakkokinsu da takwarorinsu maza wajen taka rawa da amfana da duk tsare-tsaren

cigaban mutanen karkara, kuma za a tabbatar wa waɗannan matan haƙƙoƙi haka:

(a) Su aka rawa wajen faɗaɗa da zarta da tsare-tsaren bunkasa rayuwar mutanen karkara duk kowanne matsayi:

(b) Su more wa ingantattun kayan kiwon lafiya, da suka haɗa da samun bayanai, shawarwari ko aiki a sashen tsarin iyali;

(c) Su ci moriya kai tsaye na tsare-tsaren da zai baiwa zaman takewa da jin daɗin jama'a kariya;

(d) Su sami horo da ilimi na rubutu da sana'a da yaƙin jahilci; su more wa duk sha'anin aikin gayya da aikace-aikacen malaman gona domin dai duk ƙarfafa ƙwarewarsu a fannoni;

(e) A shirya ƙungiyoyin taimakon kai da kai da na haɗin kai domin samun tattalin arziki daidai da maza ta hanyar samun aikin gwamnati ko kuma aikin kai;

(f) Su ba da gudun mawa ga duk aikace-aikacen al'uma;

(g) Su sami daman samun bashin yi aikin gona, da hanyar tallata san'arsu, fasahar da ta dace da kuma haƙƙi irin na maza a cikin sha'anin da ya shafi filayen noma da dai duk abin da ya shafi fili;

(h) Su more wa ingantacciyar hanyar rayuwa, musamman abin da ya shafi sha'anin gidaje, tsabtar muhalli, lantarki da ingantacciyar hanyar samar da ruwa, sufuri da sadarwa.

**Sashe na IV**

*Doka ta 15*

1. Kasashen da suka amince da wannan dokokin Taron zasu baiwa mata matsayi ɗaya da na maza a fannin shara'a.
2. Kasashen da suka amince da ra'ayoyin wannan Taron zasu baiwa mata dama a cikin sha'anin rayuwa da shara'a daidai da na maza kuma su basu ikon more wa wannan damar. Musamman a baiwa mata damar kammala kwangila da mallakar dukiya, kuma a ɗauke su tamkar takwarorinsu maza a cikin kotuna da kotunan tafi-da-gidanka.
3. Duk ƙasashen da suka amince da ra'ayin wannan Taron sun yarda cewa duk wata doka ta gwamnati ko ta masu zaman kansu da take tauye haƙƙin mata za a yi watsi da ita.
4. Duk ƙasashen da suka amince da ra'ayin wannan Taron zasu baiwa mata da maza haƙƙoƙi iri ɗaya a kan abin da ya shafi dokar walwalar jama'a 'yancin zabar inda zasu zauna da wurin da suke son zama.

*Doka ta 16*

1. Kasashen da suka amince da ra'ayin wannan Taron zasu ɗauki

matakan kawar da nunin bambanci ga mata a sashen aure da abin daya shafi alaƙar iyali, kuma zasu tabbatar da cewa an daidaita mata da takwarorinsu maza haka:

(a) Haƙƙoƙi aure iri ɗaya;

(b) Haƙkin zaɓen wanda suke son su aura, su yi aure kuma da amincewarsu;

(c) Su sami haƙƙi da ɗawainiya iri ɗaya da maza a lokacin aure, haka nan a lokacin rabuwa;

(d) Su sami haƙƙi da ɗawainiya iri ɗaya a matsayinsu na iyaye ba tare da la'akari da suna da aure ko basu da shi ba a lamurran da suka shafi yaransu, a duk yadda halayyar zata kasance cigaban yara dai shi ne gaba;

(e) Haƙƙi iri ɗaya da maza na shawarar yawan yaran da zasu haifa da tsara iyali, kuma su sami bayani, da ilimi, da sukunin zartar da haƙƙoƙin;

(f) Su mallaki haƙƙi iri ɗaya da maza kan sha'anin renon yara, wanda zai reni 'ya'yansu ko mallakan yaran da suke so su rena da basu da iyaye, a ƙasashen da suke da dokoki irin wannan to ya kasance ra'ayin yara shi ne kan gaba;

(g) Su mallaki haƙƙi a matsayinsu na miji da mata, da zai haɗa da haƙƙin zaɓen sunan da iyali zasu riƙa amsawa da irin aikin da zasu yi;

(h) Su sami haƙƙi iri ɗaya da na mazansu wajen mallaka, saye. guda-narwa, kula, jin daɗi da bayar da ƙaddarar da suka mallaka kyauta ko kuma su sayar da irin farashin da suke ra'ayi.

2. Alkawarin yin aure ko ba da aure da yiwa yara aure babu ruwa shara'a da haka, shara'a zata dai ƙirƙiro da doka a kan ƙarancin shekarun da ya kamata a yi aure da maida rajistar aure a wurin yin rajistar tasa doka da ta zama dole.

**Sashe na V**

*Doka ta 17*

1. Domin yin bitar cigaban da aka samu a wajen zartar da ra'ayoyin wannan Taron za a kafa wani kwamiti wanda zai sanya idanu a kan kawar da duk wani nunin bambanci ga mata (da za a iya kiransa da kwamiti), 'yan kwamitin a lokacin da za a fara zarta da dokokin wannan Taron a zaman Taron na goma sha takwas ko kuma lokacin da ƙasashe talatin da biyar suka yi Taron sanya wa wannan dokokin Taron hannu zai ƙunshi tawagar mutane amintattu da suka ƙware a fannonin da dokokin Taron suka yi magana. Za a zaɓi waɗannan

ƙwararrun ne a cikin 'yan ƙasashen da suka amince da waɗannan dokokin kuma za a yi la'akari da nahiyoyin da suka fito domin yin adalci a wajen zaɓen, da al'adu da tsarin sha'arar ƙasashe.

2. Za a yi zaɓen mambobin kwamitin ne ta hanyar jefa takardar ƙuri'a ta daga kai sai akwatin zabe a jerin sunayen da ƙasashe suka bayar. Kowace kasa zata ƙaddamar da sunan ɗanta mutun ɗaya domin a zaɓe shi cikin kwamitin.
3. Farkon zaɓen za a yi shi ne bayan wannan dokokin ya fara aiki da watanni shida. A ƙalla watanni uku kafin sabon zaɓe Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya zai aika wa ƙasashen da zasu shiga zaben takardun gayyata na su aiko da sunan mutumen da suke son ya wakilce su a cikin wannan kwamitin kada su wuce wata biyu basu aiko da sunayen ba, kuma za a tsara sunayen da aka aiko ne a daidai tsarin baƙaƙe.
4. Zaɓen mambobin kwamitin za a yi shi ne a Taron ƙasashen da suka amince da ra'ayoyin wannan Taron a hedikwatar Majalisar Ɗunkin Duniya a ƙarƙashin jagoranci Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniyar, a wannan Taron da ake bukatar kashi biyu cikin uku na ƙasashen su halarta domin isa ayi Taron (quorum), mutanen da za a zaɓa a cikin wannan kwamitin sune wakilan nan da ƙasashe suka aiko, kuma dole ne su sami ƙuri'un mafi yawan wakilai da suka jefa ƙuri'ar.
5. Wakilan da aka zaɓa zasu yi tsawon shekaru huɗu ne a wannan muƙamin, amma wakilai tara daga cikinsu lokacinsu zai kare ne shekaru biyu bayan yin zaɓen farko, da zarar an kammala zaɓen farko sai shugaban kwamitin yayi zaɓen kan mai uwa da wabi domin fitar da waɗannan wakilai tara.
6. Za a sake zaɓen wasu karin mambobin kwamitin guda biyar daidai da tanadin da sakin layi 2, 3 da 4 na wannan dokar tayi, a wurin taro na talatin da biyar na sanya wa wannan dokar hannu. Lokacin biyu daga cikin waɗannan mambobi biyar da aka ƙara zai kare ne bayan shekara biyu da zaɓen, irin zaɓen da shugaban kwamitin yayi na fitar da sunayen mutun taran nan haka zai yi domin fitar da sunayen waɗannan biyun.
7. Idan aka samu giɓi daga cikin mambobin kwamitin sai ƙasar waɗanda suka fice daga kwamitin ta bayar da madadinsu tare da amincewar kwamitin.
8. Ta amincewar baban Taron Majalisar Ɗunkin Duniya ne mambobin kwamitin saboda da muhimmancinsu Majalisar Ɗunkin Duniya zata riƙa biyan su albashi a ire-iren ƙa'idojin da ta amince da shi.
9. Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya zai samar wa

kwamitin ma'aikata da kayan aiki domin su gudanar da aikinsu yadda ya dace a ƙarƙashin wannan Taron.

*Doka ta 18*

1. Kasashen da ke cikin wannan Taron sun yi alkawarin baiwa Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya rahoton sha'anin shara'a, gundanarwa ko sai wasu matakai da suka ɗauka domin baiwa dokokin wannan Taron damar yin aiki sosai, da dai cigaban da aka samu a wannan fanni domin amincewar kwamitin:
   (a) Cikin shekara ɗaya bayan kasashen da ke cikin wannan Taron sun fara zartar da dokokin Taron; da
   (b) Aƙalla bayan duk shekaru huɗu ko kuma dai duk lokacin da kwamitin ya bukata zasu ba da rahoto.
2. Rahoton ya ƙunshi dalilai da wasu matsaloli da suka hana cika alkawarin da aka ɗauka a ƙarƙashin wannan Taron.

*Doka ta 19*

1. Kwamitin zai ƙirƙiro dokokinsa da zai bi.
2. Kwamitin zai zaɓi jami'ansa ne na tsawon shekaru biyu

*Doka ta 20*

1. Kwamitin zai yi Taron mako biyu aƙalla a cikin shekara domin amincewa da rahoton da aka bayar daidai da yadda doka ta 18 tayi tanadi.
2. Taron kwamitin za a riƙa yin sa ne a Hedikwatar Majalisar Ɗunkin Duniya, ko kuma a wani wurin da kwamitin ya amince da shi.

*Doka ta 21*

1. Ta hannun Majalisar tattalin arziki da jin daɗin jama'a ta Majalisar Ɗunkin Duniya kwamitin zai kawo rahoto ga babban zauren Majalisar Ɗunkin Duniya na aikace-aikacensa, kuma yana iya ba da shawara da amincewa da wasu abubuwa dangane da rahoto ko bayanin da ya samu daga ƙasashen da suke cikin wannan ƙungiyar. Shawarwarin gaba ɗaya ko abin da aka amince da shi ya kasance cikin rahoton kwamitin tare da tsokacin da ƙasashen da ke cikin wannan ƙungiyar suka yi idan akwai shi.
2. Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya zai baiwa ƙungiyar nema wa mata cigaba rahoton kwamitin domin su san abin da ake ciki.

*Doka ta 22*

Kafafen musamman na Majalisar Ɗunkin Duniya na da damar samun wakilta a Taron amincewa da yadda za a zartar da waɗannan dokokin

Taron a wuraren da ya shafi aikace-aikacensu. Haka nan kwamitin na iya gayyatar waɗannan kafafen musamman ɗin su ba da rahoto game da yadda aka zarta da dokokin ƙungiyar a sassan da ya shafi aikace-aikacensu.

## Sashe na VI

*Doka ta 23*

Babu wani abu daga cikin dokokin wannan Taron da zai ci karo da wani tanadi wanda ya fi dacewa domin cimma bukatar daidaita mata da takwarorinsu maza da za a iya samu a:

(a) Cikin tsarin shari'oin ƙasashen da ke cikin ƙungiyar; ko

(b) Cikin wata doka ta duniya, sulhu ko wata yarjejeniya da ƙasar ke aiwatarwa.

*Doka ta 24*

Kasahen da ke cikin wannan ƙungiya sun yi alkawarin ɗaukar matakan da suka dace a ƙasarsu domin cimma cikakken biyan bukatar dokokin wannan Taron.

*Doka ta 25*

1. Kofofin wannan ƙungiyar buɗe suke ga duk ƙasashen da ke son sa masu hannu.
2. Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya shi ne aka ɗauka ma'ajin dokokin wannan ƙungiyar.
3. Dokokin wannan ƙungiyar na iya samun gyaran fuska, kuma Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya shi ne ma'ajin kayan yin wannan aikin.
4. Wannan ƙungiyar kowace ƙasa na iya ɗaukaka a cikin ta, amma zai fara ne da ajiyar kayan da zai sanya yin hakan ga Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya.

*Doka ta 26*

1. Bukatar yin bitar dokokin wannan Taron mai yiwuwa ne a kowanne lokaci kuma ga kowacce ƙasa mai son hakan, ta hanyar rubuta takardar neman yin haka zuwa ga Babban Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya.
2. Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya shi ne zai yanke shawara a kan matakin da za a ɗauka idan har akwai dangane da wannan bukata.

*Doka ta 27*

1. Wannan dokor zata fara aiki ne kwana talatin bayan ajiyar da aka yi ga Babban Magatarkardar Majalisar Ɗunkin Duniya na kayan gyaran fuskar, ko neman cigaba na ashirin.
2. Kowace ƙasa da ke neman gyaran fuskar wannan dokokin ko neman cigaba bayan ajiyar kayan aiki na ashirin, sai a fara aiki kwana talatin bayan ajiyar kayan aikin gyaran fuska ko cigaba na wannan ƙasar.

*Doka ta 28*

1. Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya zai karɓi kuma ya rarraba ga ƙasashe duka bayanan da ƙasashe suka yi a lokacin gyaran fuskar ko neman cigaban.
2. Wani bayani da bai dace da manufa ko dalilan wannan Taron ba, ba za a amince da shi ba.
3. Ana iya jaye duk wani bayani da ake bukata, kowane lokaci ta hanyar rubuta bayanin yin hakan zuwa ga Babban Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya, shi kuma ya sanarwa duk ƙasashen da ke cikin ƙungiyar. Wannan bayanin, zai fara aiki ne tun daga ranar da aka sami rubutacciyar wannan bukatar.

*Doka ta 29*

1. Duk wani saɓani da ke tsakanin ƙasashe biyu ko fiye a kan fassara ko aiwatar da dokokin wannan ƙungiyar wanda suka tattauna suka kasa walwale wa, idan ɗaya daga cikin ƙasashen ta nemi ƙungiyar shiga tsakani ta taimaka wajen ganin an sasanta wannan taƙaddamar bayan wata shida da rubuta neman ayi hakan ƙungiyar shiga tsakanin bata sami sa'ar walwale wannan matsalar ba, ɗaya daga cikin ƙasashen na iya kai taƙaddamar a gaban kotun duniya, daidai da dokar kai magana gaban kotun.
2. Kowace ƙasa a lokacin da za a sanya wa wannan dokar hannu, ko gyaran fuska ko neman cigaba na iya yin bayani cewa bata amince da yin aikin sakin layi na 1 na wannan dokar a kan ta ba. Sauran ƙasashen ba zasu yi aiki da wannan sakin layin ba ga wannan ƙasar da tayi wannan bayanin ba.
3. Kowace ƙasar da tayi bayani daidai da ƙunshiyar sakin layi na 2 na wannan dokar, ana iya cire bayanin a duk lokacin da aka ga dama, ta baiwa Babban Magatakardar Majalisar Ɗunkin Duniya bayani a rubuce.

*Doka ta 30*

Dokokin wannan Taron da aka rubuta su a cikin harsunan Larabci, Sinanci, Faransanci, Rashanci da Sifaniyanci da aka tabbatar da inganci su, za a baiwa Babban Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya ajiyar su.

# *Nunin Bambanci Ga Mata Ya Saba Wa Akidar Daidaito Da Ta Mutunta Jinsin Bil'adama.*

Published by the United Nations Informations Centre
17 Kingsway Road, Ikoyi, Lagos, Nigeria.
DPI / 993 / Rev. 1 / WOM - December 1999